**KOMAI NISAN JIFA III**

**EPISODE 8**

**CHARACTERS**

*Tanko*

*Inna*

*Hassan*

*Husseini*

*Laraba*

*Dr. Daoud*

**EPISODE 8, SCENE 1**

**OUTSIDE HAJIYA INNA'S COMPOUND – NORTHERN KADUNA.**

**THEME MUSIC**

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **SFX:** | **LIGHT VEHICULAR TRAFFIC. SOUNDS OF DOMESTIC ANIMALS. SOUND OF TANKO MAKING HIS JUNK NOISE WITH HIS SCRAP METAL HE SELLS/TRADES.** |
| 2. | **TANKO:** | Ina kwana Hajiya Inna. Na ga kina jin dadin iskan nan mai sanyi. |
| 3. | **HAJIYA INNA:** | Ina kwana Tanko! Lafiya kayi sammako zuwa unguwar mu yau? |
| 4. | **TANKO:** | Lafiya Hajiya. Wani ne ya saida min wasu tarkace, kuma sun ce in taho da sassafe saiya sa nayi sammako. |
| 5. | **SFX:** | **CLANGING AND BANGING AS HAJIA SEARCHES.** |

6. **HAJIYA:** Wannan litilar kwan tana aiki kuwa?

7. **TANKO:** E hajiya, sabuwar kwoi kawai take bukata, da kuma kilar lakuni

8. **HAJIYA:** Bar wannan, bara in kara dubawa ko zan same wani abun sha'awa.

9. **SFX:** <u>**MORE CLANGING.**</u>

10. **TANKO:** **(CONSPIRATIONALLY)** Ehen, Hajiya, wace budurwa ce ta shiga cikin gidan ki kafin in karaso yanzu?

11. **HAJIYA:** **(THINKING)** Wacece…. Oh Laraba ce, sabuwar Nars din da aka kawo asibitin nan na al'umar mu.

12. **TANKO:** Na yi tsamanin haka, amma me take yi acikin gidan ki bayan kina waje?

13. **HAJIYA:** Anan take zama, na bata hayar dai a ciki.

14. **TANKO:** Oh na zata sabuwar matan daya daga cikin tagwayen ne ai

15. **HAJIYA:** Tanko, acikin yayana babu wanda ya sake aure, suna da matan su da yayan su

16. **TANKO:** **(JOKINGLY)** Na yi zaton kilar daya daga cikin yayan naki zai bi sawun Alhaji Bature wanda kamar yana aure da sake kowace wata.

17. **HAJIYA:** **(UNAMUSED)** Wannan wasa ne ko menene? Tanko ni bana son ka dinga danganta yayana da halin nan na Alhaji Bature na yawan aure da sake.

18. **TANKO:** **(CHASTISED)** Hajiya kiyi Hakuri, wasa nake yi

19. **HAJIA:** Toh koda wasa bana son a kwatatta yayana da mutumin nan

20. **TANKO:** Toh Hajiya, Nars Laraba daga ina take?

21. **HAJIYA:** Ban san abu dayawa akan ta ba, na dai san ya wuraren Zaria ne, amma ban takamamman garin suba

22. **TANKO:** Wato banda cewa yar Zaria ce ba ki san wani abu gare ta ba.

23. **HAJIYA:** Abu daya da na sani gamai da ita kuma shine bata da aure

24. **TANKO:** Ba Aure? Me yasa bata da aure? Kuma Hajia abin baya damun ki cewa kina da budurwa da ke haya a cikin gidan ki?

25. **HAJIYA:** Me matsallar zama da macen da bata da aure a cikin gida daya? Laraba tana da ladabi, kuma a natse take ba mu da wani matsala da ita.

26. **TANKO:** Toh, kilar baza ta jima ba aure ba, tunda za a maza daya zasu so su aure ta

27. **SFX:** <u>**BRISK STEPS COMING ON MIC.**</u>

28. **LARABA:** Hajiya, yauwa. har yanzu kina wace, na zo in karbi abu ne, zan wuce wurin aiki

29. **HAJIYA:** Toh yar uwata, allah bada sa'a.

30. **TANKO:** Sannu Laraba(**PAUSE)** Kin ga tayi kamar ba ta jiba ko, Hajiaya

31. **HAJIYA:** Kilar bata ji bane Tanko, Laraba tana da kirki kwarai

32. **TANKO:** Haka kike cewa, Amma ina ganin tana fiye girman kai, kamar mara kunya ce kuma bata sami kyakyawar tabiya daga gida ba.

33. **HAJIYA:** **(EXCLAIMS)** Tanko! Laraba bata da girman kai, tabbas bata ji ka bane, kada ka bata mata sunna .

34. **MUSIC:** <u>**BRIDGE MUSIC.**</u>

**EPISODE 8, SCENE 2**

**NORTHERN KDN, OUTSIDE HAJIA INNA'S RESIDENCE.**

35. **SFX:** **LIGHT VEHICULAR MOVEMENT. MUSIC PLAYING FROM THE RADIO. MOTOR BIKE STOPS. BRISK STEPS COMING ON MIC.**

36. **HUSSEINI:** **(CHEERFULLY)** Kai anyi zafi da daren jiya, yayi kyau dana same ka a waje

37. **SFX:** **SOUND OF STRETCHING AND SITTING DOWN**

38. **HASSAN:** Husseine, sannu da zuwa, bara in sa Jummai ta zubo maka kunu da yi dazu, zaka ji dadin sa .

39. **HUSSEINI:** Nagode Hassan, amma kada ka damu.

40. **HASSAN:** Me yasa? Zaka ji dadin shi fa.

41. **HUSSEINI:** Nasan zan ji dadin shi, amma bana son in fuskance bacin ran Asabe, indan na sha kunnun Jummai, bazan iya cin abincin da ta girka ba

42. **HASSAN:** **(LAUGHING)** Na fahimta dan'uwana. Ina son inda kuka shaku da Asabe kwanannan. Kullun kuna cikin farin ciki da jin dadi.

43. **HUSSEINI:** Kasan nine da godiya.

44. **HASSAN:** **(SURPRISED)** Ne? tayaya?

45. **HUSSEINI:** E mana, ai kune ku ka gaya mana maganan hayar tazarar haihuwa da kuke muriwa da matarka ai

46. **HASSAN:** **(LAUGHING)** Oh haka ne? bara in tuna yadda ka ji lokacin da na fada maka

47. **HUSSEINI:** **(EXCITEDLY)** Ai, kuma naga yadda hayar tazarar haihuwa da kuke amfani da ita take gamsarku, sai yasa nay i sha'awar abun.

48. **HASSAN:** **(AMUSED)** Kana daya daga cikin masu morar hanyoyin tazarar haihuwa, a'a, ba haka ba Husseini

49. **HUSSEINI:** Ah Hassan, ya taimaka ma iyali na kwarai, yanzu muna kyakyawar rayuwa a natse

50. **HASSAN:** (**LAUGHING)** Banda haka ma, farin ciki da ke tsakanin ku ya fito fili kwarai, kowa na gani ai

51. **HUSSEINI:** Gaskiya ne! muna tattaunawa ai, komai duk abinda za muyi sai mun tattauna akai

52. **HASSAN:** Abinda ya dace kenan ai, sirrin zaman aure kenan ai

53. **HUSSEINI:** Ban sani bane? Yanzu dukan wanda ke bukatar sani ina fada musu game da hanyoyin tazarar haihuwa. Kasan me ake kira na yanzu? Mallamin Hanyoyin Tazarar Haihuwa

54. **HASSAN:** (**BOTH LAUGHING)** Ina alfahari da kai kwarai

55. **HUSSEINI:** Hassan, ka taimaka ma iyali na kwarai musanman lokacin da ba wani abu tare da na keyi, nagode kwarai.

56. **HASSAN:** Mufa yan'uwa ne, tagwaye ma. Yanzu muyi Magana akan rayuwa. (**CLEARS HIS THROAT)** Husseini, an bani damar inyi takara anan al'umar

57. **HUSSEINI:** **(EXCITED)** Haka ne? ai yayi kyau, shawarar ta burge ne

~~58.~~ **HASSAN:** Amma ban fada musu komai ba tukun na, ina son in tabbatar zan yarda kafin in yi musu Magana.

59. **HUSSEINI:** Amma Hassan ai kai ka tsaba hidima anan al'umar, ina ganin takara zai zama kamar hidimar ce ta ci gaba kawai.

60. **HASSAN:** Na aminci da kai cewa ci gabar hidima ce, amma dai ka san siyasa ba gaskiya acikin ta.

61. **HUSSEINI:** Hassan ni dai ina ganin abun alheri ne fa, kuma Insha Allah z aka yi nasara.

**EPISODE 8, SCENE 3**

**HEALTH CENTRE IN NORTHERN KADUNA.**

62. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC.**

63. **SFX:** **CLINIC AMBIENCE. BRISK MOVEMENT ALONG THE CORRIDOR. CHILDREN CRIES. VOICE OF A NURSE CALLING OUT NAMES OF PATIENTS.**

64. **DAOUD:** **(CHEERFULLY)** Sannu Nars Laraba, yaya kike yau?

65. **LARABA:** Ina Lafiya Dacta Daoud.

66. **DAOUD.** Yaya kike fama anan karamar asibitin namu

67. **LARABA:** **(LAUGHING)** Ai ba karama bace, rashin lafiyar birni da na kauye daya ne.

68. **DAOUD:** **(LAUGHING)** Gaskiyan ki! Kina da wayo da hikima, wato kyau da kwakwalwa nars Laraba

69. **LARABA:** Ai ba wani abun na hikima bane. Amma nagode

70. **DAOUD:** Muna tare da shugaban asibitin dazu, ya fada min cewa wurin aiki da ki ka baro sun yaba miki kwarai

71. **LARABA:** **(SHYLY)** Na gode Dacta. na jin dadin yan kwanakin nan da nayi anan. Mutane suna tayi min kirki.

72. **DAOUD:** Nars Labara, ina ne takamaman wurin aikin kin a da?

73. **LARABA:** Daga Zaria na taho.

74. **DAOUD:** E na san daga Zaria aka kawo ki. Amma a ina a Zarian?

75. **LARABA:** Kasan dukan asibitan Zaria ne? toh daga daya daga cikin sun a taho

76. **DAOUD:** Na san asibitoci da dama a Zaria daya ke nayi karatun koyar likita a Ahmadu Bello Zaria, kuma nasan likitoci da dama dayake yawancin sum un yi karatu tare dasu

77. **LARABA:** Haka ne Dacta Daoud. Toh zan je in kula da masu jiyya

78. **DAOUD:** Oh kiyi hakuri na matsa miki Nars Laraba

79. **LARABA:** Nagode maka da kokarin da kake yin na tabbatar da na tsaba kuma na sake anan, amma dole ne in ji in yi aiki na yanzu

80. **DAOUD:** Je ki Nars Laraba, amma dole ne mu sake haduwa mu cigaba da hirar mu game da Zaria.

81. **LARABA:** Ah Dacta Daoud na tabbata aiki zayi maka yawa harm aka same damar hira, ne dai na tafi in yi aiki.

82. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE 8, SCENE 4**

**NORTHERN KADUNA. A HEALTH CENRE. AFTERNOON**

83. **SFX:** **<u>HEALTH CENTRE AMBIENCE. BRISK STEPS, KNOCK ON THE DOOR ON MIC.</u>**

84. **LARABA:** **(OFF MIC)** Shigo!

85. **SFX:** **<u>DOOR OPENS.</u>**

86. **LARABA:** Oh Malam Tanko, shigo ciki. Sunar ka ke nan ko? Abin da na gane kenan akan katin nan dake gabana

87. **TANKO:** Kin fada daidai, Sunana kenan, Nars Laraba

88. **LARABA:** **(COURTEOUSLY)** Zauna don Allah,

89. **SFX:** **<u>CHAIR IS DRAWN.</u>**

90. **TANKO:** Nagode Nars Laraba.

91. **LARABA:** Barka da zuwa yallabai, meke faruwa yallabai?

92. **TANKO:** **(SURPRISED)** Kafin in fada miki abin da ya kawo ni, bara in fada miki kin sake da yadda muka hadu a gidan Hajiya Inna dazu, na ma gaida ke amma baki amsa min ba

93. **LARABA:** Yi hakuri, abinda yasa ban gaida da kai ba saboda ban so in katse abinda kuke Magana akai tare da Hajiya Inna ba, kuma ban ji lokacin da ka gaida ni ba

94. **TANKO:** Nayi zaton haka nima, amma Hajiya Inna tace wai baki same tarbiya agida bane.

95. **LARABA:** Haka ne? Toh ka fada min abinda ke tafe da kai Mallam Tanko.

96. **TANKO:** Nars, ina bukatar taimakon ki, idan naji yin bahaya yana bani wuya kuma yana tahowa da jinni

97. **LARABA:** Oh, tun yaushe kasoma ganin allamun nan, mallam tanko?

98. **TANKO:** Yayi dan watanni nars Laraba

99. **LARABA:** Ka taba zuwa ganin likita game da hakan?

100. **TANKO:** Toh inna shan magungunan da na sayo a shago sai magani

101. **LARABA:** Amma da baka ji sauki ba, meyasa baka zo ka ga likita ba?

102. **TANKO:** ban same lokaci ba, kuma ina shan wanni maganin gargajiyan da naji ya ma wasu aiki

103. **LARABA:** Mallam tanko, ya kamata sake yin hankali, kuma ka sami kwararran shawara kafin ka sha magani, kayi mini alkawarin yin hakan.

104. **TANKO:** Naji Nars, na kuma dau alkawarin, musammman yanzu dakike nan

105. **LARABA:** Me kake nufin da haka Mallam tanko?

106. **TANKO:** Toh, na fahimci kina da kirki kuma ga kyau. Zan so in dinga samun lokacin in zo ina ganin ki

107. **LARABA:** Mallam Tanko, bana tunanin sai ka zo wuri na a asibiti akaiakai. Baka son ka yi sana’ar ka ne?

108. **TANKO:** **(LAUGHING LECHEROUSLY)** Wani dan tsuntsu ya fada min baki da aure, ina son inyi wanni abu game da hakan.

109. **LARABA:** **(COLDLY)** Mallam Tanko, ban zo nan neman miji ba, aiki ni ta kawo ni, kai ma yakama ka yi aiki

110. **TANKO:** yar budurwa kamar ke bai kamata bata da aure ba, ina ma son yadda kike da kunya ma

111. **LARABA:** Mallam Tanko, nagode da kalamai masu dadin da kake fada min, amma bani da sha'awar wani abu da wani yanzu

112. **TANKO:** toh, na gani nan ba wuri bane wanda ya dace muyi maganar nan, zan zo har gidan Hajia Inna in same ki

113. **LARABA:** Don allah kada ka zo min gida Mallam Tanko

114. **TANKO:** Zan zo Laraba, nasan kunya kike ji, yayi kyau ai ya nuna kina da ladabi ai

115. **LARABA:** Ina gaya maka yanzu fa, kada ka zo gida wuri na Mallam Tanko, kana iya tafiya ma, akwai wasu masu jiyya da zan gani

116. **TANKO:** **(ANGRY)** Ah Nars Laraba!, mara aure kamar ki? Kina korata, saboda na nuna sha'awa ta agare ki? Ba laifin ki bane ai?

117. <u>**THEME MUSIC AND END CREDITS**</u>